**Interview 1: Iliya Ado (Shugaban Sana'o'in Gargajiya, Gidan Tarihi)**

**Shugaban Sana'o'in Gargajiya**: Da ma da anka kafa ah, Di, lokacin nan sai ankace to, E *Muze*, a nan Nijer muna da tarihi. Muna da tarihi ba kad' ba ƙarami ba. Yanzu in mukabar wannan tarihi na mu mutane waɗanda za suzo na mu nabaya, ɗiyanmu da jikokinmu za sumance wannan tarihin. To minene yakamata muyi? Duka a ƙasar Niger ko duniya babu inda akayi kamar irin tsari namu na Nijar. Se sukace shi *consobolatee* yace minene yakamata muyi a nan don muyi muri ƙe wannan tarihi na gargajiya na nan Nijar?

Sai akace to, yadda za ayi yanzu agaya ma… ayi yekuwa, agaya ma dukkan mata da maza na ƙabilu kowanne ƙabila suzo za ayi, za akafa gidan tarihi. Meye gidan tarihi, me yasa za akafashi? Saboda mutane susan tarihinsu. Lokacin nan mutane sun hwara mance tarihinsu saboda mu… Nasaru sun zo sun sun yi *Kuninzam* . sun, Ee, ana cikin Mulkin mallaka Kenan wa ɗannan wa ɗanda suka tashi alokacin Nasarun nan, abubuwannan dasuka gani, Kaman shine tarihinsu. Kenan, shi kuma sun bar tarihinsu baya.

Yanzu sai akace to, wa ɗannan agaya ma mutane duka wan wannan kayanmu na gargajiya kowa yakawo tashi gudummuwa anan *Muze*, za muyi ɗakuna wannan nagargajiya, eh, kowanne kowanne ɗaki asa kayan galgajiya duka. Mata duka kowannne, wannan yakawo tsintsiyaa, wannna yakawo eh lefe, wannan tirmi, wannan yakawo duka kowanne Kaman eh *Tibawa* suka kawo irin kayansu na galgajiya… nachan ainihi. Da irin yadda suke … eh rayuwa. Sai akayi ɗaki na su. Acikin ɗaki wannan sai akasa komi da komi aka sarƙaha wani ragaya, wani wannan… komi. In kashigo ɗakin, kayan Tibawa ne. sai ankayi kran Bu… Buzaye. Buzaye suka kawo ɗakinsu… suka kawo su ma sukayi *Tant, Tuaret*. Dasukayi wannan, su ma duka aciki da wani butar shayi da wani wannan duka, akwaisu kamar yadda suke rayuwarsu wannan ta galgajiya duka ga kayansu nan.

Hausawa sai akazo su ma akayi masu ɗaki, hadda azaure da wurin dakali duka wanda ake zama yadda kika gani a *Faami*, wanda yake eh… Hausawa da wani ɗakunan wannan uwargida, ɗakunan yara, da wani wannna duka. Da wurin inda ake ɓoye mutane… Akwai wani ɗan wannna … wanda ake ɓoye yara, lokacin Nasaru…In Nasaru lokacin suna sa yara *Lakwal*. In sukazo, sai ace ma yara suhaye sama. In suka haye sama sai aruhe. In Nasaru sun zo sai ace, A'a, ai babu yaro a nan. Shikenan sai suci gaba. Yara kuma dan suje suyi noma ne. duka wannan duka akwaisu a nan.

Sai akayi kiran har lau eh mutane Za… Za… Zabarmawa da mutanen Songhai. Su ma akayi ɗakinsu daban. Duk in kashigo ɗakin wannan da wani kahensu da wani…, sai kace ɗakin Zabarmawa ne. Nan ɗakin Songayawa. Duka komi da komi akayi irin wannan na gargajiya. Mutane, radda akayi abun wannann sai shi wannan ɗin nan eh, magabatan he suka gani… A rannnan wurin ya cika, *Muze* ta cika mutane sun zo sun yaba waɗannan abubuwan. Waɗanda suke ƴan ƙabilun ma basu san waansu abubuwan ba. Saboda su an haihesu ne lokacin wannan *Kuringachuon* ɗin. Basu san wannna irin eh ga irin abinsu na tarihi ba tun chan fil azal. Kowa yayyaba wannan.

© Boston University

Yanzu dasuka yaba wannan sai akace to, Ma'iakatan kuma, akawo kowanne daga eh daga ƙabilu kowanne, in… sai adiba kamar yanzu mutanen Damagaran da aka diba sai akaga minene waɗanda suka ƙware cikinshi kuma minene waɗanda suke yi ya zame musu na gargajiya? Sai akaga aikin Hwata shine yazame musu na gargajiya domin suna yin wani *Wali* ɗin Sirdi, suna yin *Aranashiman da Shigo,* da na Raƙumi, suna yin takalma, suna yin eh Kuf, suna yin *Takfi* irin wannan na zama duka. Shi kuma wannan *Takfi* sun sa mo tarihinshi ne daga wajen Larabawa. Shi sa don suna tare da Larabawa duka….

To sai aka ɗauko Babanmu ana ce mishi Alhaji Dodo Garba. Shi ne aka ɗauko sai aka kawoshi. Shi ma bai san zama a nan ɗin, amma ana ɗan mishi wannan ɗinnan, ana ɗan mishi alheri har yasaba. Dukkanmu zuri'arshi ce mukayi. Mai aikin Laakaa shi kuma eh tarihinshi, ainihinshi kuma daga wajen Murya, tafarkon wannan wadda tafara zuwa nan daga wajen Murya aka ɗaukota ita ma Jihar Zinder. Amma shi wannan Me aikin Laakai, shi na Maraɗi ne, shi koya mishi yadda ake wannan. Su kuma aikin Laakaa lokacin nan da, … eh, … kahin Nasaru ma suzo, duk duk dasukazo ne sun iskemu da wannan aikokin na mu, na galgajiya daake yi. Masu aikin Laakaa aikinsu lokacinnan wani tukwane duka duk wanda zai ɗora tukunya lokacinnan tukunyar Laakaa ce. Kuma lokacin suna yin *architecture* irin wannan na gini. In an an ida gini sai ayi kiransu sai suzo suyi ado a bisa gini. Duk wannan aikinsu ne. Shine wannan ma'aikatan na kan wannan.

Yanzu sai mukazo, eh a lokacin nan se akwai Masassaƙa wannan. To mu acikin tarihinmu, a cikin tarihinmu na galgajiya ba mu da irin wannan *statue*. Ba mu da gumakai. Saboda tun lokacinj eh… da jimawa ƙasarmu ƙasar Musulmi ce. Amma anyi shi tun chan da, lokacin jahiliyya. To lokacin jahiliyya mutane suna aiki da gunki. Minene gunki amma gunkin na Laakaa ne ake yi. Na Laakaa ne ake yi. Ko suyi wani raƙumi irin wannna na Laakaa ko suyi wani eh, irin wannna in sukaga wani naman daji kuma anyi shi da Laakaa sai suzo susashi Kaman bisa ado kuma suzo suna bauta mishi. In Kaman mutum yamutu, wannna , wannna ɗinnan daakai, eh… ƙaton ƙarandan nan mai ɗan Kai. Sai azo asa awurin daidai kanshi. To wannan duk lokacin Jahiliyya ne. Amma yanzu Musulunci dayasauko, Masassaƙanmu suyi taɓarya, suyi turmi, suyi irin wannna kujera. Eh, duka irin wannan aikin ne suke yi.

To sai akaga sassaƙar gunkin tana da amfani bisa tarihi amma ba na mu ba . Yanzu sai yaɗauko wani *Jinyen* mutumin Guinea, ya iya sassaƙa. Sai ya ɗaukoshi sai yace mashi to, mh! Muna so, mu ka ga a nan ba mu da irin wannna aiki. Amma za musa ka tareda waɗannan na mu *Nigerien* amma dan kakoya ma yaranmu irin wannan aiki. Sai yace to babu laihi. Yace amma kahin in fara koyama waansu zan koyama ɗiyana Kenan anan wannan gidan. Sukace babu laihi ai suuma ɗiyan naka duka ana so suiya.

Yanzu sai yazo, sai akace to amma abinda zai faaraa dashi yayi duka sai aka bashi hotunaa yayi irin duka eh Kai irin wannan na… eh mutanenmu na Tarihi, na duka Kabilu duka aka gaya mai. Aka baashi hoton eh… hoton Guudumi da Guudima, yai, aka ba shi hoton Bazabarme da Bazabarma,

aka ba shi hoton Bahaushe da Bahausa, aka ba shi hoton eh Buuzuu da Buuzuwa, aka ba shi hoton eh Buuzu da Buuzuwa, aka ba shi hoton eh Bakiɗe da Baki Bakiɗaa, aka ba shi hoton Babarbare da Ba… da Babarbara, duka shi yi su, aka jera su. Yanzu haka suna nan nafarkon har a nan a *Sullaman* inda aka aje duk.

Aikin saaƙa a nan Nijar eh ya fara ne daga lokacin da mutane suna… suna noman kaaɗaa. Yanzu sai aka gaanema noman aikin kaaɗaa. Yanzu kaaɗaa shi ake gyaraata, ake eh ana nomata. Sai ake gyarata ariƙa yin saaƙa. Ana yin eh Riigunaa, ana Tufofi na sawa. Bayan Tufofi daake saaƙawa kuma sai aka riƙa yin saaƙa na adon ɗakin. Amarya yanzu in za ama macen aure, sai azo ayi saaƙa, ayi ado mai kyau. Daa Tabarma ake saawa ko Kwanoni haka Faranti asa a ɗaakunan Amaryaa. Amma yanzu sai aka gaane cewa ana iyawa ayi saaƙa, ayi wani gyaran-gyara, ayi wani eh Sakalaa, duka asa ayi ado. To, abun har yazo zauwa yanzu abun kodayake yanzu, eh aikin saaƙa sai ƙaara ja baaya yake, saboda wannan Kamfani dayawa wanda ake buɗewa nagari eh na *Mashin*. Shi yasa mu anan Nijar wanda ake saaƙawa ya fara ragewa kaɗan.

Yanzu da mu nan *Muze* muna da masaaƙa dayawa. To se kaga yaaraa, waɗanda uwayensu ke bassu son yin abin … bassu son yin saƙa ban san me yasa ba. Saboda abun, don wataran munyi tambaya sai sukace saboda abun yana ɗaukan lokaci, kahin ayi Sakalaa guda. To shi yassa suke wannan ɗin … Amma yanzu in kika diba Barkina, wani riguna, wani wannan duk da saaƙarsu suke yi da aikansu na saaƙa suke yi. Sai suyi susa. To da mu ma hakane, amma yanzu abun sai yariƙa ja baya yanzu sai ake yin *Kugartiyum*, wani gun ayi saaƙa dashi, wani gun ayi akwai abu dayawa daake yi dashi, misali. Amma yanzu wa'annan sa… saaƙa kuma yanzu sai yakomo yanzu *Specialise* ɗinshi tun chan daaka sani mutanen eh… mutanen yamma, yamma Kaman mutanen Songhai. Mutanen Songhai, Zabarmaawa, duka su ne suka shahara abisa wannan eh Sakala Sakala. Akwai *Kumtaa*, *Marnune*, *Tera-tera*, su ne duk suke yinshi.

To Maƙera na Azurfa, shi dai eh, tun eh ai ainihinshi tarihinshi, tun ainihi, eh mutane lokacin suna da kayan noma, daa a nan Nijar duka wani abun noma, da wani wuƙaƙe in muta… in mata suna aiki, duk Maƙera suke yi. Kuma eh da lokacin yaaƙi, Maƙera duk su suke yin wannan maashi, suke yin irin wannan Bindiga na galgaajiya, suke yin wani ehh, *Lakuje*, ko wannan abun cire Ciyaawaa, wannan duk Maƙera ke yi.

Yanzu lokacinda aka ce *Muze*, ana so akawo ma'aikatan Hannu. Sai aka diba aciki akwai wani shahararre anace mishi Alhaji Abba. Akwai har layau wa'ansu nan shi dai shine wanda akahi sani a nan *Muze*. Sai akayi, iya chan iya aikinshi a chan Agadez, akwai waɗanda suka fi shi aikin iya aikin. Sai akace to subada mutum guda wad wanda yaiya aikin. To saura *Latijan* sai suka ƙi tahowa sai sukace ga yi mun ba da wane. Sai Alhaji Abba mafarin zowanshi anan, aka biya mashi kuɗin wannan… Shi Alhaji Abba kawoshi akayi daga chan yanzu ake biyanshi, biya… Sauran duka waɗanda aka kawo biyansu ake lokacin nan suna aiki a nan.

Me yasanya ake musu hakannan? Dan lokacinnan sun saaba da chan wajajensu. Amma yanzu, an kawosu, an huddosu daga cikin iyalinsu, an huddo wani na Zinder, an huddo na Fesawa, an huddo na Maraaɗi, an huddo na … ah Agadez, an huddo na… ga su nan dai duk. Yanzu daaka huddosu aka kawosu, to minene yakamata aimusu? Sai ariƙa jiya musu daɗi, abasu Masauki mai kyau, abasu, ariƙa ba su ƴan kuɗi wayƴanda za susai kayan aiki. In sunyi aikinsu kuma asaya. To haka aka riƙa yi masu. Hal suka gaane zaman na su nan ya hi Alheri. Suka zaman. Duka zuri'arsu ce nan muke muke ciki.